UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FICHE PRATIQUE

# BUKATA TA MUSAMMAN: AMFANI DA ALLO DON SAMAR DA BAYANAI MASU TAFIYA TARE DA KOWA

**ZA'A IYA AMFANI DA ALLO NA FASAHA DA HOTUNA DON WALLAFA BAYANAI MASU MAHIMMANCI TARE DA AL'UMMOMI. WAƊANNAN ALLON NA IYA ZAMA HANYOYI MASU AMFANI DON AIKI TARE DA AL'UMMOMI; AMMA YA ZAKA GUJI WARE WASU RUKUNAN JAMA'A? GA WASU SHAWARWARI DON SAMAR DA BAYANAI DA AKE IYA JI DA GANI MASU AIKI TARE DA KOWA.**



**A lokacin samar da bayanai da ake ji da gani tare da kuma don al'ummomi, dole a yi la'akari da ɓangarori guda biyu don tabbatar cewa mutane masu nakasa na iya samun dama kuma su fahimci bayanin:**

- Gabatar da rubutu da zane-zane
- hidimomi wanda zai bada dama ga mutane masu nakasar ƙwaƙwalwa wajen samun bayanan dandano, ji, gani da tabawa

## MATSALAR JI

**Ya kamata kowane bayani da baki ya haɗa da rubutu. Yi tunanin sa fassarar bidiyon a lokacin shirya bayani na bidiyo.**



### Fassarar bidiyo

Fassarar bidiyo sune rubutun maganar da ake yi a bidiyo wanda yake nuna abubuwan dake kan bidiyon wanda in ba don haka ba mutanen da basa ji ko suke wahalar ji baza su iya samun bayanin ba.

Ana haɗa fassarar tare da hoton bidiyon saboda masu kallo su samu daidaituwar dama ga bayanin da aka gabatar ta murya, ba tare da la'akari ko sun samu bayanin ta murya ko rubutu ba.

### Kirƙiro fassarar bidiyon:

- Yi amfani da kalar rubutu ɗaya don nuna rubutun
- Kada ka wuce layi ɗaya ko biyu na rubutu
- Yi amfani da kalar rubutu na sans serif (kamar Helvetica) da kuma daidaita rata tsakani

- Fassarar asalin kalmomin abun da ake faɗa a bidiyon (duk da dai wata kila sai an ɗan canza wasu abubuwa saboda sauƙin karatu)
- Kuma kwatanta duk sautin da zai taimaka da fahimtar bayanin
- Yi amfani da tsarin rubutu mai kwanciya wato italics don nuna sunan wanda ke magana, muryar wadanda ba'a gani, sauti, da sauran muhimman bayanai
- Haɗa fassarar da bayanin murya
- Cigaba da daidaita fassarar akan allon
- Duba jagoran salo da kamus don tsayayyen yarjejeniya akan lambobi, dokokin harshen, alamomin da ake sawa da rubutu da yadda ake rubuta kalmomi
- Bada isasshen lokaci don karanta rubutun

### Manhajoji don ƙirƙiro fassara :

- iMovie
- MacCaption

## NAKASAR GANI

Ya kamata bayanai na bidiyo akan talabijin su hada da murya wanda yake bayyana muhimman abubuwan da ake gani. Yi la'akari da bada fassara da murya na bayanin da ake gani.

### Zama a bayyane, takaita bayani kuma da fara'a

- Yi magana a bayyane kuma a hankali yadda za'a fahimta
- Shirya kafin ka zo kuma / ko yi amfani da fassara don nuna yadda ake faɗan kalmomin
- Koyi yadda ake furta sunaye da kalmomin da ba'a saba dasu da kuma sabin kalmomi da aka amfani dasu a lokacin shiryawa

### Samar da bayani na murya:

- Yi rikodin bayanin kamar a lokacin yake faruwa kuma da kai ne
- Bayyana menene mai gani yake buƙatar sani
- Yi bayanin abun da ake gani
- Yi la'akari da abun da mai kallo ya riga ya sani

## NAKASAR KWAKWALWA

Ya kamata bayani a rubuce ya zama a tsari mai sauƙin karantawa. Bayanai mai sauƙin karantawa shima yana taimakawa mutanen da basu da ilimi sosai ko wanda basu saba karanta bayanai mai wuya.

**FICHE PRATIQUE**



## Bayanai mai sauƙin karantawa shine:

- Bayani wanda a bayyane yake kuma yana da sauƙin karantawa da fahimta
- an tsara don taimakawa mutane masu nakasar ƙwaƙwalwa su ƙara fahimtar bayanai dake rubuce
- bayanai a rubuce, da aka tallafawa da hotuna
- wanda aka amfani da kalmomin yau da kullum, ba tare da kalmomi masu wahalar fahimta ko takaitaccen kalmomi

## Samar da bayanai wanda yake da sauƙin karantawa:

- Tabbatar cewa rubutun da zane sun nuna a ɓangaren allon wanda za'a iya gani da kyau
- Yi amfani da tsarin rubutu da harufa da zai sauwaka karatu akan allon
- Yi amfani da manyan, tsarin rubutu da ake gani da kyau (misali Arial, Helvetica)
- Bada rata sosai tsakanin kalmomi
- Yi amfani da lambobi maimakon kalmomi (misali "8" maimakon "takwas")
- Zaɓi launuka da haɗin launuka a hankali
- Tabbatar akwai isasshen bambancin launi tsakanin rubutu da allon
- Zaɓa tsari wanda yake da sauƙin karantawa
- Yi la'akari da amfani da hotuna ko alamu maimakon kalmomin inda ya dace



Plus d'outils
et de conseils

pour communiquer avec les communautés sur le site : cwc.westafrica.exposed